

Karfen Bincike Na Ruhu Mai Tsarki

Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami amincewar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Mataki na farko na maganace ƙiyayya shi ne fahimtar matsalar. Da zarar ka gane ta, za ka iya magance ta. Ba kai kaɗai ba ne a cikin wannan; Allah zai taimake ka ka gane ta. Bari in ba ka misali na abin da ya faru.

A lokacin Yaƙin Duniya na II, lokacin da nake aiki a matsayin mai taimakawa likita a cikin jejin hamadar Arewacin Afirka, nayi aiki da wani likita mai hazaka. An bugi wani sojanmu da wasu fasassun ƙarafunan da bom ya tarwatsar. Sai ya zo ofishinmu da wannan ɗan raunin a kafaɗarsa. Na shirya fara aikin kula da shi, sai na tambayi likitan, "In kawo kayan wankewa don wanke raunin?"

Likitan ya ce, "A'a, ba ni ƙarfen bincike."don haka sai na miƙa masa ɗan ƙaramin ƙarfen azurfa, sai ya saka shi a cikin raunin yana motsa shi. Babu abin da ya faru a ɗan lokaci. Ba zato ba tsammani, sai ɗan ƙarfen ya taɓo ɓallin da ke ciki, sai majiyyacin ya yi ihu. Likitan ya gano matsalar.

Lokacin da na sake tambaya ko in kawo kayan wankewar, sai likitan ya amsa, "A'a, kawo mani dai abin cirewar." Sai ya saka abin cirewar ya kuma ciro ɓallin karfen. A daidai wannan lokacin ne yake so a wanke raunin.

Wataƙila kana ɗan wanke ciwon da yin ayyukan addini a kan raunin da ba zai iya warkewa ba saboda akwai wani abu a cikin sa da ke sa shi ya yi ta ruruwa. Amma, idan za ka buɗe zuciyarka ga Ruhu Mai Tsarki, to, zai bayyana tushen matsalar. Idan ƙarfen bincike na Ruhu Mai Tsarki ya taɓo wani ɓallin, kana iya yin ihu idan ya zama dole, amma kada ka yi tsayayya da shi! Ka roƙe shi ya yi amfani da ƙarfen cirewa domin ya cire matsalar. Daga nan ne, Allah zai sa wani abin da zai warkar da raunin maimakon a riƙa ɗan lallaɓa shi na ɗan lokaci.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa ina buɗe zuciyata ga ƙarfen bincike na Ruhu Mai Tsarki don bayyana tushen matsala ta. Yesu ya ɗauki ƙiyayya ta don in sami amincewar Sa a wurin Uba. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-143-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.